# FADAKARWA

## A kan: Kasuwanci da dabarun sai da kaya

## Kashi na 5a: Wasu abubuwa hudu na kasuwanci mene ne kasuwanci?

Kasuwanci wata hanya ce ta yadda jama'a ko kungiyoyi zasu iya biyan bukatunsu ta hanyar musanyen kaya ko wasu abubuwa da junansu. Watau kasuwanci wani abu ne wadda ya ke lura da gano bukatun jama'a domin biyansu ta hanyar samun karuwa ko riba.

### Muhimman abubuwa hudu na kasuwanci

Wadannan abubuwa hudu da a ka lissafa a kasa sune abubuwan da kasuwa ta dogara a kan su, idan suka yi kyau, kasuwa ta yi kyau, idan kuwa suka baci, to ba magana

1. Hajja
2. Farashi
3. Mazauni
4. Talla

### 1. Hajja

Hajja itace abin da a ka kasa domin sayarwa ko kuma wani aiki da za a iya yi domin samun karuwa. Hajja ta dogara ne a kan bukatun jama'a masu sayayya. Wadannan bukatu suna iya canjawa lokaci-lokaci.

A ko wane lokaci, ya wajaba masu sayar da kayan noma su kasance da cikakken sani a kan amfanin hajjojinsu, yadda a ke amfani da su da kuma lokacin amfaninsu.

Yana da matukar mahimmanci ga masu sayar da kayan noma su san wadannan abubuwa game da kowacce hajjarsu:

- Irin hajja.
- Abin da hajja ta kunsa.
- Yadda a ke amfani da hajja.
- Amfanin hajja.

### 2. Farashi

Farashi shine abin da mai sayayya zai biya kafin a bashi hajja ko a yi masa aiki. Farashin kayan ya dogara ne a kan:

- Yadda a ka yi shi.
- Ingancinsa.
- Wadatarsa a kasuwa.
- Karfin aljihun masu saya.
- Farashinsa a hannun sauran yan kasuwa.

## 3. Mazauni

Mazauni;, watau wurin da dan kasuwa yake gudanar da harkokinsa muhimmin abu ne a kasuwanci. Mazaunin dan kasuwa shi yake nuna irin abin da ya ke sayarwa.

Kafin dan kasuwa ya zabi inda zai kafa kasuwancinsa, ya kamata ya yi tunanin:

- Daga ina zai sayo kaya domin kasa wa?
- Ina za a kai kaya idan an saya daga wurinsa?
- A ina suto dinsa na ajiye kaya yake?
- Yaya fuskar wannan wuri take ga jama'a?
- Yaya harkar sufuri take zuwa wannan wuri?

## 4. Talla

Talla shine sanar da jama'a samuwar kaya da kuma kokarin jawo hankalinsu su saya. Talla ya na lura da ra'ayin masu sayayya, abubuwan da su ka fi sha'awa da kuma a inda suke zaune. Amma yawan talla da tasirinsa ya dogara ne a kan kokarin dan kasuwa da kuma karfin aljihunsa.

Talla ya kunshi:

- Sanar da jama'a samuwar kaya kai tsaye.
- Sanar da jama'a samuwar kaya ta hanyar rediyo, talabijin da jarida.
- Nuni da wasan kwaikwayo a kan ingancin kaya.
- Takara da bayar da kyaututtuka a kan sayen kaya.
- Tsare-tsare na musamman na jawo hankalin jama'a su sayi kaya.